Kamin Aydaaan yayi magana ne Abban Ibadan ya karbe maganan da cewa " Nine na je na amsan masa Auren  Aydaaan.!
*#Mmn teddy**Don Allah don darajar Allah ki taimake Ni kar ki fitar mun da Wannan littafi ,

kema Don Allah kar ki karanta mun Indai baki biyani Haƙƙi na ba , Idan kin karanta baki biyani ba Wallahi keda Allah , Don banga Tsadar shi ba da Zaki kasa cire kuɗi ki saya ,Indai kina iya siyan Data na WhatsApp ,to kam tabbas zaki iya cire ₦300 dai ki saya littafin The Sexxies House ƙaramin group kenan , Vip group₦500 SPC ₦1000 via 6037312299 Mohammed A'isha keystone bank ko katin MTN ta Wannan number 08081202932 .*

Yauwa Jama'a na ,ku ƙwantar da hankalin ku , inshallah ko bamu kammala littafin nan kamin RAMADHAN ba , zamu cigaba da yin sa ina posting bayan An sha Ruwa , Don haka masu cewa Mmn teddy ayi da yawa Ramadhan ya kusa ,mun san kamin ramadhan zakice kin gama ...a'a Indai bamu kammala ba Ni nayi maku Alƙawarin cigaba da posting har mu gama inshallah. Jiya kuna ta jirar night update ban samu nayi ba ,ayi mun hakuri Don ALLAH .
17

Alh.Abubukar.! Kaine ka amshi Auren Aydaaannn ɗin ? A yaushe kenan? Kuma Auren shi da Wacce Yarinyar? . Hajiya Rahina Tayi maganan cikin Jin Zafi , Don dama ita burin ta bai Wuce ta ga Ranan da Yar nata Ɗaya Tilo zata Auri Aydaan ba , Don tafi burin ganin hakan fiye da ita ƴar nata , A cewan ta Aydaaannn suruki ne Wanda zata nuna shi cikin bajinta ga Hajiyoyin Ƙawayen ta . Mom Rahina macace Wanda take idon ta a bude a yage ,Wani Abun da take yi ko ƴaƴan cikin ta basa yi , Don ce masu Sumayya take yi Yan Ƙauye , To Wannan Kaɗan ne daga Rayuwar Hajiya Rahina , Wani zafi take ji akan maganan Abban Ibadan , zuciyar ta na tafasa kaman ruwan Tafasa . Hajiya Barmani ce cike da Karaya don Alh Abubakar shine ɗan ta ƙarami , don haka Sosai take Ɗaga masa ƙafa . Cikin Muryar su ta tsofaffi tace " Abubakar , Aure kaje da kai akayi mawa Aydaan ? Kaima kaman ƙaramin Yaro.?

Daddy ne ya amshi maganan tare da cewa " A'a Ni ban yarda da Wannan maganan ta Alh Abubakar ba , Har yaushe akayi haka ,duka duka yaushe ya dawo ƙasar ? . Shi dai Aydaan tun da ya faɗa masu yana da mata bai kuma cewa komai ba sai kamewa yayi ,ya na koma masu wannan mugun miskilin , duk maganan da suke yi bai ce uhm ba , Zuciyar sa babu Abun da yake tunano masa sai Jidderh , yanzu ya zanyi da Ita?.
Muryar Abban Ibadan ne ya katse su yana cewa " Hajiya kuyi hakuri ,kar ku ga laifin Aydaan , Nine na yanke komai , kuma nima ba naje da zummar na yi hakan bane ,sai dai ALLAH ya rubuta dama a uku ga Watanan Aydaan zai Auri Aaliyah . Nisawa Abba yayi tare da kallon Daddy , Da kuma sauran yayyun nasa ,kamin ya cigaba da cewa " Aydaan shine Wanda yazo Airport a ranan da na dawo daga China ya Ɗauke Ni muka dawo Gida . So nasan yanda yake , duk da shi ba mai yawan magana bane ba , amma a yanayin sa na fahimta aƙwai Abun dake damunsa , Wannan yasa Ni Muna dawo Gida ,daga Ni Sai shi na tambaye sa meke damun sa?. Bai ji nauyi ba ya fayyace mun Lamarin sa Akan Yar Aikin sa Wato Aaliyah , Ya ƙare maganan hankalin sa a tashe don baya jin zaku amince da maganan auren ta , domun of course yasan auren Gida za'a yi masu don ya faɗa mun , Ni ne na yanke Hukuncin zuwa Garin Yobe da ƙafa na kuma ba tare da nayi shawara da Kowa ba . Bayan na isa Yobe , tabbas dangin Yarinyar suna cikin talauci da zafin Rayuwa , mahaifin ta mai karamin karfi ne , Aydaan baya Wurin lokacin da na yanke hukuncin daura masu Aure ,don neman Auren kawai naje muyi maganan da Iyayen ta ,amma a yanayin condition din da na tadda su ,sai na yanke hukuncin a ɗaura

Auren nan take .  Na kira Aydaaannn na kuma tambayar sa yana son Yarinyar ga Abun da na yanke akan su .... Hajiya Tun da nake ban taɓa Ganin farin cikin Aydaaannn irin na Wannan Rana ba ...Wannan yasa nan take aka tara mutane da Sauran dattijan unguwa aka kuma ba Aydaaannn Auren Aaliyah nan take . Hummm Numfasawa Abba yayi tare da cigaba da cewa " Hajiya Kar mu manta Halin da Aydaan ya shiga a sanadiyar So a Wancen Shakarun baya , Da yaya muka samu kan sa? Idan Bamu haɗa da da Wacce yake So ,to wacece zata bashi kular da ya dace?. Afuwan Bisa jin Wannan maganan tawa nasan na ɓata .... A'a Ya isa Abubakar , Babu komai shikenan ,zan rarrashi Sumayya tayi haƙuri su zauna su biyun ,tun da haka shima Aydaaannn ɗin ya so.!

Hajiya Barmani tayi maganan tana Kallon Inda Sumayya take ,idanun ta na fidda Hawaye ,don har ga Allah bata jin zata iya zaman kishi da wata akan Aydaaannn , Dole sai tasan yanda zata yi don Taga ita kaɗai ta mallake shi . Miƙewa Summy tayi ba tare da tace mawa kowa komai ba ta tsallaka tana ficewa daga Falon . Girgiza Kai Hajiya Barmani tayi tana cewa " Allah sarki ,kun gani ko? Itama maganan bai mata dadi ba gaskiya , gayi nan kuka take yi , Aydaan zamuyi magana dakai yanzu ku tashi kuje Allah yayi ma rayuwar ku albarka . Amin suka furta tare da miƙewa suna barin Part ɗin Hajiya Barmani .

***

A farfajiyar Gidan ne Aaman ya kalli Aydan tare da cewa " Aydaan ka huta Zaka ji dadin rayuwar ka ,Cox zaka Auri cikakkiyar mace , akasin mu da zamu Aura Ragowar mu . Kallon sa Aydaan yayi duk da yana cikin wani irin yanayi marar Dadi , Amma sai yace masa " Kaman ya kenan? Ai kai ne wanda kafara Kauda budurcin Hibba ,don haka don ka Aure ta ba laifi bane ai . Girgiza Kai Aaman yayi tare da cewa " Bani bane , Cousin Mubarak ne , Kuma a yanzu wani zafi nake ji tamkar na....shiru yayi da maganan idanun sa na kadawa yana yin Jah ,takaicin duniya ya gama isar sa . Cak Aydaan ya tsaya yana jin maganan Aminin nasa har cikin Zuciyar sa . Ganin yanda hankalin sa yake a tashe yasa Aydaaan riko Hannun Aaman yana cewa " taho muje ka rani wani Wuri . Kallon sa Aaman yayi tare da cewa " Mu je to " . Moton sa ya shiga tare da fara reverse yana ficewa daga Gidan. Ina zaka je da Wannan Ranan? . Garin su Kano. Kano..! Aaman ya maimaita tare da kallon Aydaan ,me zaka yi acan?. Ba tare da Aydaaannnnn ya kalle sa ba ya basa amsa da " Wurin Jidderh zani . Aydaaannnnn.! Aaaman ya kira sunan sa tare da masa Alamun ya haƙura mana ,Amma kuma Aydaaan kallon sa baiyi ba ,don shi abun da yasa ma ransa sai yayi yake Samun nutsuwa .

***

Kallon Su Ammiee Da su Abba Hajiya Barmani tayi kamin tace " To kune iyayen Wannan yaran , ya kuke ganin Al'amuran zasu kaya? Yanzu waye Zai rarrasar mun Sumayya ?. Shiru Ammiee tayi kamin tace " Hajiya Hakuri ya zama mata Dole , tun da babu yanda Zamuyi Aure ya riga anyi , Yanzu Ni zan samu Sumayya mu rarrashe ta . Sauke Ajiyar zuciya Hajiya Barmani tayi kamin tace " To ai yanzu dole ayi Ɗaya , Aydaaannnnn ya fara tarewa da Matar nasa da ya

Aura ,kamin tarewar sa da Sumayya , Wannan a ganina zai fi samun masa zaman lafiya ,akan ace an kai masa matan duka rana Ɗaya . kallon ta Abba yayi tare da cewa Hajiya kaman ya kenan? .

Ina nufin ko yau ko gobe ko jibi a tabbatar Wancen yarinyar ta tare a gidan Aydaan , Don nan da Sati Guda za'a ɗaura Auren duka yaranan babu fashi ....*Don Allah don darajar Allah ki taimake Ni kar ki fitar mun da Wannan littafi , kema Don Allah kar ki karanta mun Indai baki biyani Haƙƙi na ba , Idan kin karanta baki biyani ba Wallahi keda Allah , Don banga Tsadar shi ba da Zaki kasa cire kuɗi ki saya ,Indai kina iya siyan Data na WhatsApp ,to kam tabbas zaki iya cire ₦300 dai ki saya littafin The Sexxies House ƙaramin group kenan , Vip group₦500 SPC ₦1000 via 6037312299 Mohammed A'isha keystone bank ko katin MTN ta Wannan number 08081202932 .*

18

Kallon Hajiya Barmani duka sukayi ,kowa na tsoron abin faɗi ciki har da Ammiee da ta tsaya tana kallon Daddy ko zai ce Wani Abun ,amma kuma sai yayi shiru .... Ganin Hakan yasa Ammiee sauke Muryar ta ƙasa tana cewa ' Hajiya Don Allah ayi hakuri ,A hada Tarewar Aaliyah da Na Sumayya duka , Ai shi ba ƙaramin Yaro bane , shekara Talatin ai yayi hankali , Yasan abun da ya dace , Idan muka yi duba Hajiya ga iyayen Aaliyah ba ƙarfi ne suke dashi ba , kamata yayi a sanar dasu iyayen ta....Ya isa Haka.! Hajiya Barmani tayi maganan tare da Ɗaga mawa Ammiee Hannu . Ko su shirya ko basa shirya ba ,dama Wani Abin kirki zasu iya taɓukawa ?.  To bari kuji Ina Alh Abubakar?.

Cikin Sauri Abban Ibadan yace ' Na'am Hajiya.! bana so da buƙatar ganin an kawo mana Komai koda cokali ne na cikin Wannan Gidan ,kana Jina?. Kana Jina? . Saurin girgiza Kai yayi tare da cewa ' Ina Jinki Hajiya , inshallah Ba za'a yi hakan ba ,Ni ai a matsayin mahaifin ta nake , Don haka Ni na Ɗauki nauyin komai na Aaliyah tamkar Mahaifi gare ta ".

Taɓe Baki Hajiya Barmani tayi tare da cewa " Kaji dashi dama kaine ka kulla komai , ku tashi kuje Allah ya kara maku arziki da Wadata . Amin suka furta ,jiki a sanyaye kowa ya bar Falon Hajiya Barmani tare da nufar Part ɗin shi . Gaba Daya Hajiya Rahina ranta babu daɗi , jin zafi take tare da ji kaman taje ta ƙarar da Dangin Aaliyah da ita da kowa nata ,sai taga Ƙarshen Auren , Aydaan Mutuwa zaiyi idan bai Aure ta ba. A haka ta isa Bangaren ta ,Wanda da isan ta kai tsaye Bedroom Ɗin Summy ta nufa .

Sautin kukan ta ne ke tashi a hankali , Yayin da ko ina na jikin ta Rawa yake Alamun Zazzaɓi mai zafi ya kamata , Cikin Sauri Hajiya Rahina ta nufi Inda Sumayya ke ƙwance ta kululluɓe gaba Ɗaya Jikin ta har zuwa kan ta . Summy ta.! Momy Rahina tayi maganan tana kai hannun ta tare da Saurin yaye Blanket ɗin da Summy ta rufu dashi .

Ohhh Momy Sanyi nake ji , Momy ki rufe Ni." Summy ta ƙare maganan tana ƙanƙane Jikin ta , Hawaye na cigaba da fin Kuncin ta .!

*Kuyi hakuri guntun night update 🥱*
*#Mmn teddy*.!*Don Allah don darajar Allah ki taimake Ni kar ki fitar mun da Wannan littafi , kema Don Allah kar ki karanta mun Indai baki biyani Haƙƙi na ba , Idan kin karanta baki biyani ba Wallahi keda Allah , Don banga Tsadar shi ba da Zaki kasa cire kuɗi ki saya ,Indai kina iya siyan Data na WhatsApp ,to kam tabbas zaki iya cire ₦300 dai ki saya littafin The Sexxies House ƙaramin group kenan , Vip group₦500 SPC ₦1000 via 6037312299 Mohammed A'isha keystone bank ko katin MTN ta Wannan number 08081202932 .*

19

Ɗaga Hannu Momy Rahina tayi tana shafa Gyefen Saman Goshin Sumayya ,kana tace " Sannu bari yanzu na Kira Family Doctor Ya duba jikin naki da lafiyar ki duka?. Bana Buƙatar Family Doctor Mom , Yau kema da bakin ki kince Family Doctor? Sanin kan ki ne tun ba yau ba ,bana taba yarda Ko mun Rashin lafiya ,wani Doctor ya duba Ni ,in dai ba Aydaaannnnn ba. Summy tayi maganan tana kallon Mahaifiyar nata tare da matso Hawaye , Kamin ta haɗiye Ɗaɗɗatan Yawu tana cewa " Mom Yau A gaban kowa Aydaaannnnn yace baya Sona, Baya Son Aure na baya bukata na ke nan yake nufi A rayuwar sa? Momy Ƴar Aikin sa yake So , Humm kuma yar ba kowa ba . Mom bazan taba Warkewa ba daga ciwo nan sai dai na samu Sauki , Idan kin ga Na Warke to Aydaaannnnn ya cire Soyayyar ko wacce mace ya aje a gyefe ya dauki nawa Soyayyar da matuƙar muhimmanci.... Nisawa Momy Rahina tayi tare da cewa" Ya isa Sumayya kiyi barci ,kamin Aydaaannnnn ya shigo , bana Son duk Wani abu da zai ɗaga miki Hankali , Amma Ni nayi miki Alƙawarin ganin Bayan Auren Aaliyah da Aydaan ke da ma ko wacce mace da yake buri...ko da anyi Auren Aaliyah Wallh da makirci sai ta bar Gidan Aydaan .

Aydaan mijin mace Ɗaya ne Wato Ke .! Bayan Sumayya shida mace sai kallo . Wani irin Sanyi Summy taji Dadi na mamaye Zuciyar ta . Momy kin tabbata?. Gyaɗa Mata Kai tayi tare da sakin Murmushi tana Cewa " Inshallah Sumayya,zaki gani .

**

Yobe
Yammacin wannan Rana Aaliyah ce zaune tana aikin yankar kuɓewa , Inna Turai ne ta iso gaban ta tare da cewa " Aaliyah aje yankar nan ki taho Malam na Son magana damu shi da baban ki Salihu.  Haka kurum taji ƙirjin ta ya buga ,gaban ta na yanke wa tare da Faɗi , Inna lafiya dai ko? . Aaliyah bana ce ba , Tun da nidai muje muuji Kirar . Amsan kubewan Inna tayi tare da aje shi a kitchen tana yin gaba Aaliyah na bin ta a baya suka isa Ɗakin Abba . Bakin Su

dauke Da Sallama suka shiga dai dai Baba Salihu da Abba na amsa nawa Inna Turai da Aaliyah . Tsugunawa Aaliyah tayi har ƙasa tana gaishe da Baba Salihu kamin ta koma ta nade Gyefe tana jirar jin musababbin kiran nata .

Aamm'amm Baba Salihu yayi gyarar murya tare da kallon su su duka yana fara faɗa masu dalilin Kirar nasu . Da farko Inna Turai ,Kiyi haƙuri ,kece Uwa ga Aaliyah ,amma munyi Abin da Bamj nemi shawarar ki ba a matsayin ki na Uwa gareta . Itama kuma Aaliyah Batasan da Wannan Abu ba . Abun ya kuke ne shi yasa har muka ga ya zama wajibi a yau a yanzu mu sanar maku ,don ku fara shirye-shirye .

Kallon sa Inna Turai tayi cikin Rashin fahimta tace " Babu komai Malam Salihu me ya faru fadi muna jinka.!

Humm a gaskiya Mun bada Auren Aaliyah ga Aydaan Moddibo tsawon sati Uku kenan da Faruwar komai . Wani irin tsoro ne da Firgicin ya dirar ma Aaliyah ,wanda ya sata Ɗagowa da Sauri tana ware idanun ta akan na Baba Salihu... Inna Turai kuwa Cikin ɗaga murya tace " Ban gane ba , Me kuka nufi? .  Abba ne ya amshi zancen tare da yi masu bayanin yanda auren nata ya kasance , tare da kara basu haƙuri ,daga karshe ne yake sanar masu da cewa " Jibi Dangin Aydaan suka shaida zasu taho a tafi da Amarya .

Malam Wannan wani irin Aure ne? Shin neman kai muke da Aaliyah? Haba Wannan anya .....Haba Turai haba da hankalin ki? Cewan Baba Salihu kamin ya cigaba da cewa " Addu'a ya kamata kiyi Allah ya albarkaci Auren ,ba Wai ki na rinka Wannan zancen ba . Aaliyah ne da tuni idanun ta suka tsinke da Hawaye , Shi kenan Na Auri Ƙwarto marar imani , Na ƙare rayuwata a gidan Harijai ,gidan Ƙwarata.....!

Naji kuna ta maganan ba tayi morning update ba ,to a gaskiya ban dade da dawowa school ba gashi muna shirye-shiryen fara yi ma yara Exam , wannan yasa kuka ji Ni shiru , ga kuma Ɗan aikace² na Gida , Amma kuyi hakuri da Wannan Zuwa anjima zamuyi mai tsawo sosai .
#Mmn teddy*Don Allah don darajar Allah ki taimake Ni kar ki fitar mun da Wannan littafi , kema Don Allah kar ki karanta mun Indai baki biyani Haƙƙi na ba , Idan kin karanta baki biyani ba Wallahi keda Allah , Don banga Tsadar shi ba da Zaki kasa cire kuɗi ki saya ,Indai kina iya siyan Data na WhatsApp ,to kam tabbas zaki iya cire ₦300 dai ki saya littafin The Sexxies House ƙaramin group kenan , Vip group₦500 SPC ₦1000 via 6037312299 Mohammed A'isha keystone bank ko katin MTN ta Wannan number 08081202932 .*

Hawaye ne ya cigaba da zuba mata babu kakkautawa , wanda Ganin haka yasa jikin su Abba yin Sanyi ƙalau . Cikin Muryar rarrashi tare da ban hakuri , Abba yayi Kirar sunan Aaliyah tare da cewa " Mama na, Kin San komai nayi miki ,Ni Mahaifin ki ne bazan yi Abin da zai cutar dake ba da rayuwar ki....Ina mai Addu'ar inshallah Zaki samu kulawa da Kwanciyar Hankali tare da Aydaaannnnn . Kiyi Haƙuri....Saurin share Hawayen idanun ta Aaliyah tayi tare da ƙaƙalo Murmushin Dole duka don ta kwantar mawa da Abba da Hankali ne tace " A'a Abba Na sani Abba duk Abin da kayi ka yanke akai na Abba baxaka cutar dani ba ,koda kuwa ya zama illa wannan haka Allah ya ƙaddara , Abba Zanyi biyayya na amince ba zance A'a ba . Kai Alhmdlh , Allah yayi miki Albarka mai Sunan Mama . Malam Salihu yayi maganan cike da nuna matsanancin Farin cikin shi bisa ga Aaliyah.

Shiru Inna Turai tayi tana kame hannayen ta ,domin jikin ta yayi sanyi ,ita bata san Abun yakai ga Haka ba . Miƙewa Aaliyah tayi tare da cewa " Abba zan iya tafiya?. Cikin Sauri Abba yace " Tafi Aaliyah Allah yayi miki Albarka . Amin Inna Turai ta amshe sa , Yayin da Aaliyah ta juya tana ficewa daga Ɗakin Abba tana nufar madafi.

Bayan fitan Aaliyah ne Inna Turai ta kalli Su Abba tare da cewa " Amma dai kun bin cika nasaban Wannan gida ko? Ni dai Wannan Auren ... Kar ki tada Hankalin ki Turai , Inshallah Allah zai basu zama lafiya tsakanin su .numfasawa Inna Turai tayi tare da cewa " Okay to shiknnn Allah y tabbatar mana da Alheri.  Amin y rabbil alamin . Ɗakin ya amsa .

***

Tun da ya shiga Layin Su Jidderh ,ya ke tunano Abubuwa da dama wanda suka faru tsakanin su a shekarun baya . Lumshe ido yayi Yana bin ƙarƙashin biyar dake gaban gidan su Jidderh da kallo . A hankali ya fara tuno da zuwan shi kofar gidan na Farko ....Hauwa Jubi ki ƙatuwar ki dake shekaru kusan 18 babu miji ,sa'o'in ki duka sunyi Aure amma ke kin rantse sai kin yi boko ,ba kya hakura da Secondary school din ba hakan nan ? Cewan Baba yana cigaba da banbami . Jikin Hauwa ne yayi Sanyi , Shiru tayi tana kasa magana...Wuce ta yayi yana cewa " Kar ki manta Ni zan iya aura maki kowa nayi niyya sai naga karshen Son Boko ko duniya ....! Sauke Ajiyar zuciya yayi dai dai Aaman na yin parking tare da kallon Aydaaannnnn da ya dawo daga Duniyar tunanin sa da ya faɗa . To yanzu ya ake ciki? Wa zai kira mana ita Jidderh? . Kallon Aaman Aydaaannnnn yayi ba tare da ya bashi amsa ba ya fito daga Moton yana nufar hanyar Gidan su Hauwa . Biyo bayan sa Aaman yayi dai dai suna jin banbamin Baba a inda yake cewa " Ai tun da kin ki zaman Aure , sai ki fita fanfo a buga miki ki debo mawa Iyayen ki Ruwan Albarka .

Wani irin bugawa Ƙirjin Aydaaannnnn yayi yana jin Zafin Maganan Baba , Wai dama har yanzu bai sauya ba? Bai daina wahalar mun da Jidderh ta ba?. Fitowa yayi Hauwa na bin sa a baya hannun ta Ɗauke da bokitin ƙarfe . Saurin zubewa suka yi tare da cewa " Sannu Baba suna

gaishe da Baban Hauwa . Maimakon ya amsa su sai tsayawa yayi yana tafka wani irin salati tare da cewa " Dama tun da naga Hauwa ta fito nasan ka buga ganga ne jujaliyar ta ka ya fito mun da ita daga Ɗakin mijin ta .

Wai kai Wani irin sheɗanin yaro ne? Ka hana mun ya sukuni tana budurwa ,yanzu ma a dakin mijin ta sai da kasa ta fito . Cikin Wani irin murya Hauwa ta kalli Su Aydaan da mamakin ganin su ya gama kai ta karshe . Aydaan kune?. Tayi maganan tana aje bokitin cikin wani irin yanayi . Kamin suyi mata magana ne Jidderh tace " Aydaaannnnn ka gani ko? Wallahi Ni nasan haƙƙin ka ne ke bibiya ta, Aydaan...... Ke Rufe mun baki koma ciki , Baba ya katse Jidderh dake fashewa da kuka . A yau zan sa a kira Salisu ya koma dake gidan sa .bazan yarda da Wannan shashashun yaran ba .!

Idanun Aydaaannnnn ne suka kaɗa ,hannun sa har Rawa yake na ɓacin Rai . Wanda Ganin haka yasa Aaman kama shi yana cewa " Aydaaannnnn mu wuce , ma dawo next time". Ran sa a ɓace baya jin komai sai sautin kukan Jidderh......!

Gn*Don Allah don darajar Allah ki taimake Ni kar ki fitar mun da Wannan littafi , kema Don Allah kar ki karanta mun Indai baki biyani Haƙƙi na ba , Idan kin karanta baki biyani ba Wallahi keda Allah , Don banga Tsadar shi ba da Zaki kasa cire kuɗi ki saya ,Indai kina iya siyan Data na WhatsApp ,to kam tabbas zaki iya cire ₦300 dai ki saya littafin The Sexxies House ƙaramin group kenan , Vip group₦500 SPC ₦1000 via 6037312299 Mohammed A'isha keystone bank ko katin MTN ta Wannan number 08081202932 .*

Suka nufi Moton yayin da Baba ya banzama yayi na cikin Gida ransa a matuƙar ɓace , Tun daga Zauren Gidan yake Faɗin ,daga Fitowar ki Hauwa shine har kin Sanar masa yazo ku cigaba daga inda kuka tsaya? Dama Ni tuni nake zargin ki Hauwa ,yau kuma gashi zargi na ya tabbata .  Banda iskanci yau ko ma Saki uku Salisu yayi miki ai idda kike yi , shine zaki fara Kula wasu maxan . Subhanallah Malam mai kuma ya faru? Umma tayi maganan tana Ɗagowa tare da kallon Baba da ya sauke Wular kansa yana sababi . Ina Hauwan take? Yayi maganan ba tare da yaba Umma amsa ba . Hauwa.! Ya fara ƙwaɗa Kirar Hauwa Ransa a matuƙar ɓace . Saurin fitowa Hauwa tayi jikin ta Ko ina Rawa yake yi na tsoro , Zubewa tayi hawaye na bin Kuncin ta , cikin matsanancin kuka take fadin " Baba Don Allah kayi Hakuri , Wallahi ban san waya faɗa mawa Aydaaannnnn wani Abu ba, Kuma bana  tunanin yasan komai dake tsakani na da Salisu . Rufe mun baki Shashancin Banza da Wofi , bai sani ba yazo kofar Gidan nan yau ? Rabon shi da Gidan nan shekara nawa? Eiyee?? Tun lokacin da kikayi Aure tsawon shekaru goma bai kara saka ƙafarsa a kofar gidan nan ba ,sai yau tun da kina shirin zama bazawara . Hauwa ki sani Aydaaannnnn ba zai taba Auren ki ba , saboda yafi ƙarfin ki ,yaudara ce kawai ta ya'yan masu kudi ,ya gama dake ya barki Fanko . Haba Malam haba malam ... wannan Abun naka yawa yake yi Wallh . Me kike nufi to me ƴa? Naga dai bake kika haifi Hauwa ba, Hauwa

jini nace don haka kome zanyi akan ta kisa mun ido .

A'a gaskiya saka idon yayi yawa , Gaskiya na gaji , Hauwa fa Allah ne ya bamu it....Wayyo Umma don Allah kuyi hakuri,kuyi Shiru Umma .... Hauwa tayi maganan tana Rushewa da matsanancin kuka tare da cigaba da cewa " Baba zan koma Gidan Salisu ,wallahi zan roƙesa . Kinji maganan gaskiya nan , Baba yayi maganan yana cigaba da muzurai .

***

Kai Aaman Kar ka tafi bazan iya barin Ƙofar Gidan nan ba tare da na ji Muryar Ta ba , Ina Son Jidderh , Don Allah ka dakata , zata fito Ni Na sani . Dakatawa Aaman yayi daga Driving din da yayi niyya ,cike da jin matsanancin Tausayin Ƙanin nasa Ya ce" Aydaaannnnn Kana Son Hauwa ,Amma kuma tun farkon Rayuwar ka bata taɓa nuna maka So ba ,sai Wahala....Me ya kawo Aaliyah nan? Muryar Aydaaannnnn ya katse Aaman wanda shima yayi saurin juyawa Yana kallon inda Aaliyah take tsaye tare da mai adaidaita . Sallamar mai adaidaita tayi tana ɗaukar Ghana most go ɗin ta tare da nufar Gidan Su Hauwa . Innalillahi wai'inna ilaihir raji'un me take anan? Me ke shirin faruwa ne? . Abun da Aaman ya furta kenan wanda kamin yayi magana Aydaaannnnn ya fice daga Moton yana nufar inda Aaliyah take cikin Sauri da sassarfa .

Caraf taji an riƙo Hannun ta wanda yasa Aaliyah saurin juyowa tana kallon bayan ta , Waro ido waje tayi tare da masa Kallon nashiga Uku . Aaliyah.! Ya kira sunan ta cikin wani irin sanyi ,wanda tun da take bata taba ganin sa a irin Wannan yanayin ba." Yallaɓai Aydaan me nayi maka? Har nan ma ka biyo NI? Aaliyah Aaliyah Jidderh ta?. Wani irin kallo tayi masa kamin tace " Wacece Jidderh kuma? Don Allah Aydaaannnnn ka rabu dani , Meye ka Ɗauke Ni wai? Ni Bazan Aure ka ba shi yasa na Taho gidan Wan mahaifiya ta , Saboda Nasan shi da halin sa idan ya tsaya akan Gaskiya babu mahalukin dake dakatar dashi duk kudin ka duk girman ka . Tsayawa Aydaaannnnn yayi yana juya maganan Aaliyah a kan sa ....kamin ta fixge hannun ta tana wuce shi da sauri . Keee .! Ya kira ta a gadarance da izza . Ni mijin ki ne kin manta ne ko sani ne baki yi ba? Ai aure an riga anyi shi ,saura tarewa nan da kwana biyu.  Naga mai hanani tafiya da matata ....!
#Mmn teddy
#morning Update*Don Allah don darajar Allah ki taimake Ni kar ki fitar mun da Wannan littafi , kema Don Allah kar ki karanta mun Indai baki biyani Haƙƙi na ba , Idan kin karanta baki biyani ba Wallahi keda Allah , Don banga Tsadar shi ba da Zaki kasa cire kuɗi ki saya ,Indai kina iya siyan Data na WhatsApp ,to kam tabbas zaki iya cire ₦300 dai ki saya littafin The Sexxies House ƙaramin group kenan , Vip group₦500 SPC ₦1000 via 6037312299 Mohammed A'isha keystone bank ko katin MTN ta Wannan number 08081202932 .*

Cak ta ja ta tsaya , wani irin murmushi ya saki tare da cigaba da cewa " Sannan magana ta gaba , wannan maganan da kika faɗa mun zaki maimaita mun shi nan da ƙwana biyu sai kin maimaita gani ga ki ....Kallon sa tayi rasa Abun da zata ce masa abun ka ga yarinta kawai sai ta fashe da kuka tana cewa " To kawai yanzu gani Yallaɓai ka kashe Ni ka huta dama haka kake so . Ai tun tuni ka faɗa mun idan muka yi Aure Wahalar dani zaka yi .... Shiii ya zaki rinƙa ihu haka ,a kan hanya kaman ba mata da miji ba? Yayi maganan yana mata wani iri kallo na kin san Sauran ,sai kuma ya cigaba da cewa " matsowa kusa Zaki yi , amma idan ba zaki iya ba ai ba wani Abu bane ,Ni sai na matso kusa da matata ... Yayi maganan yana matsowa daf da ita ,har suna jiyo daukar numfashin juna . Yauwa ko kefa Nur Albi . Ko da mijin ki ya ɓata miki rai har rungume sa zaki iya yi ba wani damuwa ba ne ? . Wani irin kallo tayi masa A hasale don ta lura ya maida ita kaman yarinya yar shekaru tara , wannan yasa ta a zafafe cewa " Kaman ya kenan ?. Kamin ta rufe baki dama neman hanyan da zaiji Sanyi a zuciyar sa yake yi , ita dai ji tayi ya sa hannun sa yana jawo ta jikin shi tare da Rungume ta yana sauke ajiyar zuciya da cewa " Kaman haka mana ,sai Kiyi ta mawa Aydaaannnnn ɗin naki kukan shagwaɓa Ni kummm....jan ye jikin ta tayi da Sauri tana waiwaigawa gyefe² kar yazo Wasu sun gansu masu wucewa . Kallon sa tayi tana buɗe Baki zata yi magana ,sai kuma ta rasa me zata ce masa ,kawai sai ta fashe da Kuka .... Saurin sa hannun sa yayi yana Warewa tare da cewa " Oya Come lemme Hug you...! Da gudu ta juya tana shigewa Gidan ,tana jin Muryar sa yana cewa ' Ki gaida mun da Baba .

Aaman dake can Jikin Moton su yana kallon duk Wani Abu da ya faru tsakanin su , Dariya yake yi sosai kaman zai kifa a sarari yana furta " Aydaaannnnn you're d arrogant boss , Wallahi kana damun ƙanwata da Yawa fa?. Murmushi Aydaan yayi yana jin Sanyi a zuciyar sa , duk damuwar nasa ya nema ya rasa . Sau da yawa yana mamakin kan sa ,a kowani irin hali yake ciki ,yana ganin ta ko jin Muryar ta yayi sai ya nemi ɓacin Ran nasa ya rasa. Kwazin mu Wuce mu koma gida ." Gida kuma? Ai na dauka yanzu Gidan su Amaryar mu muka nufa? . Murmushi yayi yana sa hannun sa tare da shafa Sajen fuskar sa tare da cewa " it's remain 2 days a kawo mun ita gida na , naga Karshen Tsiwan nan nata . Dariya Aaman yasa kamin yace " To don Allah Abi ta a hankali, I know you very well, Nasan yanda kake gurzar mata , kake masu caka² ,amma wai duka su Momy fa har yanzu Ganin na Allah suke maka . Kallon sa Aydaaannnnn yayi yana sakin Murmushi tare da lumshe Lulun idanun sa yana buɗe su a hankali , babu Abun da yake Hangowa sai a ranan da aka kawo masa Aaliyah gidan sa . Bazan manta da Wannan Ranan ba.! Yayi maganan yana kallon Aaman da suna haɗa ido su sun san Yaren nasu , Kecewa Da wani irin Dariya suka yi ,wanda tun da nake ban taɓa Ganin sun yi irin ta ba .

Mu tafi Yanzu Please , naga Kirar Ammiee yanzu. Okay so you can call her back so that muji dalilin Kirar nata ko?. Kirar Numbern Ammiee Aydaaannnnn yayi inda buga daya biyu ta ɗauka cikin Muryar dan tashin hankali ,wanda daga Ji yasan babu lafiya yaji tana cewa " Aydaaannnnn kana ina ne? Kazo Gida yanzu yanzu don Allah.! Cikin Sauri ya furta " Ammiee lafiya? Meke Faruwa?. Humm numfasawa Ammiee tayi kamin tace " Lafiya ba lafiya ba , Sumayya ce babu lafiya ,kasan ciwon ta ,kuma taki yarda kowa ya duba ta sai kai wai zaka Duba ta. Wannan wacce irin yarinya ce mai masifar taurin kai ? Taurin kan nata har a lafiyar ta ma sai tayi shi?. Akul Aydaaannnnn Sumayya fa nace maka ba Hibba ba? . Sumayya yayar

kace kake kira da yarinya? . Kallon sa Aaman yayi da duk yaji mai ke faruwa shi da yake Gyefe . Alama yayi masa da ido akan yace gasu nan isowa yanzu . Wanda hakan Aka yi , I'm sorry Ammiee , yanzu zamu taso . Datse Kirar Ammiee tayi yayin da Aydaaannnnn ya kalli Aaman dake kallon sa shima .

Amma fa kai dan rainin Wayo ne 🙄 Summy ce Yarinya , saboda zaka Aure ta ko? Allah mun gode maka da baka fito a babban mu ba , da wannan mulki naka da Son girma mun shiga uku . Murmushi Aydaaannnnn yayi kamin yace " Ƙwazin yi sauri kasan bata da lafiya tun ba yau ba . Fara barin layin suka yi kamin Aaman yayi duba ga Aydaaannnnn yana cewa " Amma me ya kawo Aaliyah gidan su Jidderh?. Dan taɓe baki Aydaaannnnn yayi kamin yace " Ban sani ba ,Amma zan sani nan gaba inshallah .

**

Aaliyah..! Aaliyah Abba ya fito daga Ɗaki yana Kirar sunan Aaliyah ,wanda Inna Turai tayi tsimi ta rasa bakin magana don ta lura Aaliyah bata cikin gidan nan ,kuma tasan a halin da ake ciki babu inda zata je da Ya wuce gidan Umman Hauwa . Ina Aaliyah take ne? Abba yayi maganan yana kallon Inna Turai , kamin tayi masa magana ne ƙaramar Wayar sa ta fara ruri , duk da yayi mamakin ganin sunan mai Kirar ,amma a haka ya daga cikin faraa tare da cewa " A'a Malam Barka da Rana . Barkan ku dai . Kamin Abba yayi magana Baba ne yace " Aaliyah tana nan Wuri na ,babu mai mata Auren dole . Ƴa tace ". Murmushi Abba yayi tare da cewa " To to Malam , Yanzu bani  Aaliyah muyi magana . Cikin zafi Baba yace ita kadai nake Gani na tuna da Mahaifiyar ta ,don haka ba zaku kashe ta ba itama . Jinjina kai Abba yayi yana dannewa tare da cewa ' Haka ne Malam kaba Aaliyah muyi magana . Aaliyah Ƙarana kika kai ? , To ki dawo Gida . Shine Abun da Abba yace tare da katse Kirar . Tsayawa Inna Turai tayi tare da cewa " Malam Aaliyah zata dawo dai ko? . Shiru Abba yayi kamin yace " Inshallah .

**

Ɓangaren Aaliyah kuwa bayan rabuwar ta da Aydaaannnnn , Da gudu ta shiga Gidan Baba tana Cin karo da shi yana sababi , Hauwa tsugunne , Umma itama na sharce Gumi . Nufar Hauwa tayi da Gudu tana faɗawa Jikin ta tare da cewa " Adda Hauwa ,Adda Hauwa nayi..... Kasa ƙarike maganan tayi ganin Baba a tsakar gidan . Hauwa ne ta Ɗago Aaliyah cikin Sauri tana shafa fuskar ta tare da cewa " Aaliyah ta meke Faruwa? Kukan me kike yi?. Kamin Aaliyah tayi magana ne Baba yace " Kema idan kishiyar Uwar taki ta dame ki tattaro kayan ki ,Kiyi zaman ki anan . A'a Malam ba'a yi haka ba? Ba fa muji meke damun ta ba ? Kuma yanzu Turai ta sauya ,tana  Son Aaliyah da duk jinin Abba a yanzu . Umma tayi maganan cikin Sanyi , Aaliyah me ya faru? Ta tambayi Aaliyah cikin nuna kulawa . Umma Auren dole Su Baba Salihu suka Ɗaura mun da Wani .... Aure.??? Baba yayi maganan cikin ɗaga Murya , ina wannan bazata saɓu ba.!
#Mmn teddy*Don Allah don darajar Allah ki taimake Ni kar ki fitar mun da Wannan littafi , kema

Don Allah kar ki karanta mun Indai baki biyani Haƙƙi na ba , Idan kin karanta baki biyani ba Wallahi keda Allah , Don banga Tsadar shi ba da Zaki kasa cire kuɗi ki saya ,Indai kina iya siyan Data na WhatsApp ,to kam tabbas zaki iya cire ₦300 dai ki saya littafin The Sexxies House ƙaramin group kenan , Vip group₦500 SPC ₦1000 via 6037312299 Mohammed A'isha keystone bank ko katin MTN ta Wannan number 08081202932 .*

23

Baba ne ya kalli Aaliyah yana cewa " Tayaya zasu yi miki Auren Dole , idan suna taƙama su iyayen ki ne ,nima matsayin Uba nake a wurin ki koda bani na kawo ki Duniya ba . Malam ka bar wannan zancen don Allah , Aaliyah faɗa mana ke kin san yaron ne ? . Kallon Umma Aaliyah tayi kamin tace " Eh na san shi ,aikatau nayi a cikin Gidan su ,har part ɗin shi ma ... Nan Aaliyah ta fara basu labarin Aydaan , Wanda tun da tace Gidan Moddibo Hauwa ta fahimci Wane ne . Shiru tayi tana jin Wani irin yanayi tsikar jikin ta na tashi . Sai da Aaliyah ta gama maganan ne Baba ya dafe kai yana cewa " Wannan tabbataccen Yaron Suka Wanke ki suka miƙa masa? Tabbas zaki dawo ba'a hayyacin ki ba Aaliyah , kuma Indai ina da Rai ba tare da amincewar ki ba bazan taba yarda a miƙa ki gidan Aydaan Moddibo ba . Tsayawa Aaliyah tayi tana Son tambayar Baba dama yasan Aydaan ne ? Sai kuma tayi shiru tana nazarin kalaman sa.  Ita dai a wannan lokaci taji yana mawa Abba Sababi ne ta Wayar sa , wanda kamin tayi Aune taga ya mika mata Waya suna magana da Abba . Jiki a sanyaye ta mike tana cewa ' Baba Bari na koma.! A'a Aaliyah ki taho dakin Umma ko ruwa ki sha kamin ki tafi . Wani irin kallo Baba ya watsa mawa Hauwa , Wanda tayi Saurin kasa da kan ta . Kama Hannun Aaliyah tayi tana shigewa Ɗakin Umma da ita .

Aaliyah ne da shigar su ta fara neman wurin zama ,wanda kamin ta zauna Hauwa tace " Ke dakata.! Bana kirawo ki bane don ki zauna ... Aaliyah kalli idona ki faɗa mun matsayina A wurin ki . Cike da mmkin sauyawan Hauwa Aaliyah idon ta na cikowa da Ƙwallah tace " Ke Adda ta ce , Yaya na Uwa ɗaya uba ....ya isa ban tambaye ki wannan ba . Kin san da hakan ? Hauwa tayi maganan tana kallon Aaliyah wanda tayi saurin gyada Mata Kai . Motsa Baki Hauwa tayi tare da fara cewa " ke da Bakin ki a kwanakin baya kika taho kika same ni da cewa " Na faɗa miki duk wani Abu da zai ɓata mun rai game dake ,domin ki kiyaye ,nace miki babu komai, To Aaliyah yanzu Akwai . Na'am Adda Hauwa me nayi miki? Aaliyah tayi maganan tana narke mata ,domin tana Gab da fashewa da kuka . A'a bance kimun kuka ba , Aydaan .! Ki sani idan kika kuskura ko sau Ɗaya kika ɓata ma Aydaan tamkar Ni Hauwa kika yi mawa , Haka idan kika guje shi kusani tamkar Nine kika guje mawa." Aaliyah idan kika azabtar da Aydaan Wallh bazan yafe miki ,ki fita ki bani Wuri Kiyi duk Abin da kikayi niyya .

Fashewa da Kuka Aaliyah tayi kamin ta juya da Gudu tana ficewa daga Ɗakin ko sallama ba tayi mawa su Umma ba ta fita tana kuka . A hanya sam kan ta ya kulle ,me Adda Hauwa take nufi? Shin tasan Aydaan ne? a'a Babu ta yanda Za'ayi Tasan shi . A haka ta isa gida ,tana shiga Ta nufi Ɗakin Abba . Zubewa tayi har ƙasa tana basa Haƙuri tare da cewa " Na tuba Abba , na

amince Wallh zan masa biyayya zan zauna da Aydaan ,amma kuce Adda Hauwa ta daina fushi dani Don Allah. Inna Turai ne ta riƙo ta tana cewa " Ita Hauwan ke fushi dake ? Gyada Mata Kai tayi tana fashewa da Sabon kuka . Dafa ta Inna tayi tare da shafa bayan ta tana rarrashin ta ya isa . Zata daina kinji?.

Saurin riko Hannun Inna Turai tayi tare da cewa " Inna Adda da gaske zata daina fushi dani? . Gyaɗa Mata Kai Inna Turai tayi tare da cewa " Ai kin san bata taɓa fushi dake ba , Yau ma dai ta nuna miki kisan darajar Auren ki ne . Mu tafi ɗaki muje kici Abinci . Miƙewa Aaliyah tayi Abba na Murmushi cike da jin sanyi a zuciyar sa ta fice daga Ɗakin tare da nufar Ɗakin Inna Turai .

**

Basu samu isa Garin Ibadan ba sai Safiyar goben ranan . Koda suka isa Gida Kowa part ɗin shi ya nufa tare da kimtsawa ,kana kusan Awa biyu Aydaaannnnn ya fito yana nufar Ɓangaren Ammiee . Anan ne take ƙara Sanar masa da Isowan Amaryar sa a gobe , Wanda Batasan Tuni Abban Ibadan ya sanar masa ba . Ammiee ne tace dashi yaje ya duba jikin Summy ,don har yanzu jikin nata sai a hankali ,ciwo sosai take yi . Jin hakan yasa shi nufar part ɗin Hajiya Rahina . A Falo ya tadda Momy Rahina don saukowar ta kenan daga Bedroom din Summy . Hannun ta dauke da glass cup da alama ruwa ta bata sannan ta fito . Washe baki yayi cike da jin dadi da faharin ya zama sirikin ta tace " dawowar yaushe ?.. murmushi yayi yana gaishe ta kamin ya haura upstairs don nufar bedroom din Summy .

Da shigan shi Bedroom din ya ga ko ina ta rufe ruguf , a hankali ya taka yana nufar window tare da yaye labulan , Tun shigowar sa taji ƙamshin turaren sa ,wanda a ko'ina taji bazata yi makowar mai shi ba . Wani irin Raɗaɗi take ji tana ɗago idanun ta tare da Ware su daƙyar dai dai yana isowa.  Hannun ta ta ɗago masa tana miƙa masa , Wanda a hankali ya miƙa nasa yana haɗawa da nashi ,tare da matsowa kusa da ita yana hayewa saman gadon ,dama sun saba. Matsa hannun nata yayi a hankali yana jin Zafin jikin nata yayi tsanani . Ɗago da Lulun idanun sa yayi yana zuba su a kan fuskar ta , wanda suna haɗa ido tafara zubda Hawayen da suka dade da daskare mata a zuciya . Kuka take sosai har dasu Ajiyar zuciya . Wanda duka yasan dalilin yin masa hakan ,bai wuce kishi da bakin cikin Auren sa da Aaliyah . Kallon ta yayi yana cewa " Meke damunki Summy? Ina ke miki ciwo ? . Ɗago da idanun ta tayi da suka yi Jah kaman zata masa magana sai kuma ta kasa . Please ki faɗa mun ? Me yasa kika ƙi bari a kaiki asibiti?. Aydaaannnnn ina Son ka.! Bazan iya jurar ganin nayi kishi da ko wacce ya ma ce ba ,zan iya komai , bazan iya kishi da Yar Talaka ba kuma abun Haushin ma yar Aiki na.!

Kuma yar Aikin gidan mu .! Wani irin ba dadi yaji , wannan yasa shi yi mata Wani irin kallo kamin yace " Nine nace ina Son ta ai , so ina ke miki ciwo?. A Maimakon ta basa amsa kawai sai ta fashe da kuka ,nasani ai . Aydaan ka tsane Ni me nayi maka? . Ke  Summy , Wai ke bakya duban Ni Ƙannin ki ne? Me yasa zaki Soni? .So babu ruwan sa da Wannan , Amma zaka iya kashe Ni ta hanyar yimun Allura yanzu ai kai likita ne ."  Kallon ta yayi cike da jin dan tausayin ta . Hannun sa yasa yana Rungume ta jikin sa , wanda nan naga Abun mamaki shigar

da kan ta tayi saman ƙirjin sa tana shaƙar ƙamshin jikin sa tare da masa Wani irin kuka can ƙasa² na tada Sha'awar masoya . Sarai tasan waye Aydaaannnnn shi yasa duk wani Abu da zata ja hankalin sa take yi . Hannun sa yasa yana shafa suman kanta har zuwa Bayan ta tare da hura mata iska a Gyefen kunnen ta a hankali ,is Okay my Summy ,ya Isa ina Son ki kema . Sauke Ajiyar zuciya tayi tana saka hannun ta tare da shafa saman ƙirjin sa tana wasa da ƙwantattun gashin ƙirjin shi . Lumshe ido yayi tare da saurin riƙe hannun ta cikin wani irin yanayin murya yace " Stop it". Yayi maganan tare da miƙewa yana cewa " Bari na Dauko first aid box na yi miki allurao . Ga shi nan ai , Ammie tun juya ta shigo dashi .

Juyawa yayi yana kallon inda ta nuna masa , nufar wurin yayi yana dubawa tare da Ɗaukar Wasu alllurai yana haɗawa wuri guda tare da jan shi a ƙaramin sirinji ....Takowa yayi zuwa inda ta miƙe zaune . Tsayawa yayi yana kallon ta , kamin yace ' Bani Hannun ki nayi miki?. Kallon sa tayi a shagwaɓa tace " A'a Ni ba'a mun Allura a hannu kamun a baya kawai . Cike da yagewar ido da yafi nata yace " Okay juya ,kuma kar ki mun raki . Juya masa tayi yana sa hannun sa tare da Sauke Skirt ɗin jikin ta , Wani irin abu ya haɗiye , hannun sa yasa yana shafa tudun Bayan ta , Kusan mintuna biyar yana kasa sa Sirinjin . Ita ko lumshe ido take , tana fara jin tana tsiyaya . Wani irin magana take a harde kaman wanda ake saka mata shocking . Aydaaannnnn Please... Please Aydaaannnnn , Aydaaannnnn ...! Hannun sa yasa yana shafa Gadon bayan ta cikin Wani irin Salo ,yana jin yanda Alƙalamar sa ke harbi kana yace " Mun kusa saura kwana nawa ne ? Just mu kara hakuri kar muyi sabon Allah . No Aydaaannnnn Babu komai fa . Kai ai miji na ne zaka zama . Wani irin kallo yayi mata bai san lokacin da ya zura allurar ba tana gantsarewa tare da sakin yar ƙaramin ƙara . Hannun sa yasa yana lailaya mata kamin yace " zan Aiko miki da magani ki tabbatar kin sha . Yayi maganan a gadarance kun dai san shi da isa da mulki ga uwa uba Miskilancin hummm. Juyawa yayi yana ficewa da ga Bedroom din tare da nufar Farfajiyar gidan .

***

Tsawon dare Aaliyah ta kasa barci ga damuuwar Adda Hauwa ga kuma damuwar daga Yau gobe Ibadan aka kuma yi da ita . Me yasa Adda Hauwa zata Faɗi mun haka ? Me yasa abun da bata taba mun ba ?. saurin miƙewa Aaliyah tayi daga Zaune tana faɗin Wallhi na gane na gane yanzu . Adda Hauwa itace Jidderh n da yake magana , tabbas itace ,saboda yace muna kama ba kaɗan ba .... Dafe kai Aaliyah tayi tana rushewa da kuka mai taɓa zuciya. Shine wanda Adda Hauwa zata yi fushi dani akan sa , Wayyo Ni Aaliyah , Me yasa Zaka shigo mun rayuwa ta . A haka ta wuni tana kuka har aka fara korar sallar subahi .

**

Kaman yanda Aaliyah idanun ta suka gagara rintswa haka ɓangaren Aydaaannnnn ,duk dashi na farin ciki ne ,duk ya kosa safiya tayi a taho masa da Matar sa ,wanda yake ganin Abun tamkar a mafarki . Sai bayan ya dawo sallar subahi sannan ya rintsa , inda a barci mai dadi ya

dauke sa . A cikin barcin sa ne yayi mafarkin Aaliyah ta haifa masa cute bby girl , Wanda sukayi kama sak har daƙwa²n idanun . A haka ya tashi cikin matsanancin Farin ciki , Privacy ya nufa don lokacin ƙarfe Goma na safiya . Bayan ya kamala karin kumallo sa ne , ya mike tare da nufar Ɓangaren Ammiee Anan yake jin tun Safe An tura Jirgin yawo Heliƙwafta na malam bahaushe don dauko Amarya . Hajiya Barmani tace bata buƙatar Ganin dangin Aaliyah ko mutum daya ,wannan ne yasa Momy Rahina Da Momyn Aaman su kadai tafiya don ɗauko Amarya , jirgi suka bi don zuwa Garin Yobe.... To ko ya abun xaya kaya.....!
#Mmn teddy*Don Allah don darajar Allah ki taimake Ni kar ki fitar mun da Wannan littafi , kema Don Allah kar ki karanta mun Indai baki biyani Haƙƙi na ba , Idan kin karanta baki biyani ba Wallahi keda Allah , Don banga Tsadar shi ba da Zaki kasa cire kuɗi ki saya ,Indai kina iya siyan Data na WhatsApp ,to kam tabbas zaki iya cire ₦300 dai ki saya littafin The Sexxies House ƙaramin group kenan , Vip group₦500 SPC ₦1000 via 6037312299 Mohammed A'isha keystone bank ko katin MTN ta Wannan number 08081202932 .*

24

Nufar Ɓangaren Hajiya Barmani Aydaan yayi don Abba ne ya kira sa yana Sanar masa da Abun da bai san dashi ba sai a Wannan lokacin ...Wai Hajiya Barmani ta ce " Ba za'a kai Aaliyah Sabon Estate din su ba , Anan Gidan Zata zauna a ɓangaren sa.  Wannan yasa Shi nufar Ɓangaren Hajiya Barmani , inda da Shigar sa ya tadda Summy Hibba , da Sauran ƴammatan Gidan . A'a Aydaaannnnn Ango na . Kallon Hajiya Barmani yayi kamin yace " Waye Angon naki? . Murmushi Hajiya Barmani tayi kamin tace " To ƙwarai ni kuwa , Don babu Abun da zaka nuna mun ƙuruciyar ma na Fika. Ran sa ba Dadi ya shigo Falon nata ,amma jin Wannan maganan nata yasa shi Darawa tare da cewa " Humm To Ni Angon Aaliyah ce. Saurin kallon sa Sumayya tayi yayin da Hajiya Barmani tace " Akul kar Wannan ya ƙara fitowa daga Bakin ka na haneka Kul". Kai Angon mata biyu ne , Yau dai za'a Fara kawo wacce kake kallon ta a mata , don Ni nasan Waye Talakawa da mugun abu ,babu Mamaki an gama da kai ne ,an kai sunan ka an tsaface ka Allon Ƙarfe .  Ɗago da Lulun idanun sa yayi yana sakin mawa Hajiya Murmushi bawai don bai ji zafin maganan nata ba a'a . Sumayya itace Ƴar gata kuma Ƴar dangi ƴar uwar ka ta jini ba Wancen abun ba da ba zata taɓa nuna .... Hajiya Don Allah ki bar wannan maganan .! Ni bashi ya kawo Ni wurin ki ba ". Ƙwazin.! Hibba ta kira Sunan Aydaan cikin Sanyin murya tana Ɗago da idanun ta tare da kallon Aydaaannnnn . Ina jinki ,yayi maganan yana Bin fuskar ta da kallo .

Ƙwazin Wannan Abun da kake is not Good , Bai dace ba , Anty Summy tana Son ka ,me yasa kake kokarin fifita Soyayyar Ƴar aikin mu akan na jinin ka? Mun taso tare , Tun muna yara muke So da ƙaunar junan mu , but Why now zaka ce baka Son jinin ka ko nace kana fifita wacce Da ita da Dabbobin gidan nan basu da mara ba . Don dabbobin mu sun fi mana ita amfani , su ko ba komai zamu yanka muci Namar su tayi mana Dadi. Ita kuwa fa? Sai dai ƙarin Ɗawainiya da Jidali iyaye.....Keeeee..! Ya Wani daka mata gigitaccen Tsawa wanda tun da take dashi bai taba masu irin wannan Tsawan ba ,don ko ina na Wurin sai da ya amsa . ina Wasa dake ne?? Ni sa'an Wasan ki ne? , Saurin girgiza Kai Hibba tayi tana kokarin sa kuka , Kamin yayi magana ne

Summy da ta gama tunzura tace " Saboda An kawo aibun ta shine kake Wannan maganan ? Ai maganan Hibba gaskiya ne , Nima kamin Tsawa amma sai dai ta tsaya iya nan don babu duka ". Saboda me kika ce haka? Yayi maganan yana maida kallon sa ga Summy dake farfar da ido na musifa . Saboda Ni Yayar kace ,bakai ne ka riƙe mun hannu ba a yarinta, nice Wacce na kama hannun ka kana yaro mu tafi makaranta , Aydaaannnnn baya na ya goya ka ba sau Ɗaya ba Sau biyu ba... Soyayyar ka jarabta ta ne a gare Ni ...a kullum bani da burin da ya wuce na ganni tare da kai , amma kai da yake butulu ne mai manta alheri , kasha faɗa mun baka SO na sau nawa ? . Me yasa me yasa Aydaaannnnn duk matan duniya ka rasa wacce zaka hada Ni kishi sai Aaliyah?? .

Saboda Ina Son ta , kuma ba zan daina Son Aaliyah ba har ranan da zan ban doraar duniya , saboda ina jin ta tamkar jini na dake gudana cikin jiki na.' Hajiya Aaliyah zasu sauka a yau a cikin gidan nan ,amma ban yi Alƙawarin zan barta takai gobe ba ,ba tare da na Kaita Gidana . Yana Gama Faɗin haka kamin Hajiya Barmani tayi magana ya juya fuuuu yana barin Falon .... Zuciyar sa na masa Wani irin Zafi ...zaki maimaita ke yayata ce ,tabbas sai kin maimaita wannan kalmar , Kuma zaki sha mmkin Waye Ni Aydaaannnnn , baki Sanni ba har yanzu.

Bayan fitan sa ne Hibba ta kalli Summy tana cewa " Anti Summy you make a mistakes , Maganan ki yayi kaushi da yawa ,kin san Fa Waye Ƙwazin? Baya da kirki ,baki masa ba ma yayi miki bare kin masa . Na tausaya miki kar ki manta yau saura kwana nawa ne ? . Ni nafi So Aydaaannnnn ya kashe Ni na bar duniyar na Huta . Jin Haka yasa Hajiya Barmani cewa " A'a fa , sam duk bata kai ga Hakan ba Sumayya , Ni dai kawai abu daya zaki mun yana miki abu ki rabu dashi , idan kin zo ki faɗa mun ,zanyi maganin tijarar Wannan yaron , Rashin kirkin Aydaaannnnn yayi yawa , daɗi na dashi Daya shine yawan Sadakan shi da Tausayin marasa Ƙarfi . haɗa ido duka suka yi sai kuma suka yi shiru a zuciyoyin su kowa na fadin " Baki san Waye Shi Ɗin bane , Ai dole ya rinƙa Wanke zunuban sa da Sadaka ."

**

Ɓangaren Aaliyah Kuwa Tamkar ba Amarya ba ,babu ado babu gayun nan na Amare , Kuka take tun da Suka taho har suka Sauka . A ganin ta wannan ba Aure aka yi mata ba sayar da ita kawai akayi ma Aydaan . Haushin Ahalin yanzu da kuma tausayin kan ta take yi , Don bata san wani irin tsana suka yi ma Talaka ba sai a yau , Sun ɗauke ta tamkar baiwa haka suka ce Babu wanda zai biyo ta a dangin ta wai daga baya mai bukatar ganin ta ya zo . Tuno da nasiha n Abba da kuma na Inna ,Umma ya sata cigaba da rera kukan ta a hankali , Gyefe guda na zuciyar ta tana faɗin Na shiga Uku na . Don tun da take kukan Su Hajiya Rahina Momy Muhibba Babu Wanda Ya tankata har suka sauka a farfajiyar Gidan .... Umman Mubarak ne da Ammie suke a farfajiyar Estate din don anan Heliƙwafta Nasu ta sauka da misalin 7pm . Sunan garin yayi duhu ne amma kuma ko ina na harabar gidan tamkar Rana yake haske ya haskaka ko ina . Cikin Sauri Umman Mubarak ta ƙariko tare da kama Aaliyah , Eyyya Come on Baby shiiiii..... It's Okay Dirling . Ta ƙare maganan tare da rungumo Aaliyah jikin ta tana rarrashin ta tare da shafa bayan ta . Tun yaushe take kukan ne ? Umman Mubarak tayi maganan tana kallon su Hajiya Rahina ,wanda ta tabe baki ,Momyn Hibba ne a takaice tace " A haka muka

same ta ,muka kuma dauko ta . Oh ...! Ya isa kewan Gida ne ,kin san Abun ka ga Yaro . Umman Mubarak tayi maganan cike da Gogewa Don duk matan gidan ta fisu Gogewa da sanin duniya . Ita da yake ƴar siyasa ce don shekara daya kenan da saukar ta a kujerar sanate , don haka ta saba haba² da Al'umma talaka ko mai kuɗi . Murmushi Ammie tayi tare da cewa " To ko a kira Aydaaannnnn ne ? . Cikin Sauri Umman Mubarak ta amshe ta da Cewa " Of course yess, Saboda tafi sanin sa ƙila shi ya rarrashe ta tayi shiru .

Haushi ne ya kama Momyn Hibba nan take tace " Don Allah ku bar  yaro ya huta ,kar ku manta yanzu fa suna can suna kujiba² na Auren su saura ƙwana shida ne , So ai ita ba ƙaramar Yarinya bace sai kace Hibba ,ko Hibba zan kai Ɗakin Aaman ba zata yi ya kukan nan ba haba Don Allah.! Caraf Hajiya Rahina ta amshe da cewa " Tare mun da hanya yar Gari haba . Ammie ne ta kalle su kamin tayi magana Umman Mubarak tace " Hibba tafi shekara ashirin da biyar , Wannan fa ko Ashirin bata hada ba She's not up to 18yrs yarinya ce ƙarama ƙarama kuwa . Don Allah dai kawai ku bar wannan maganan , yanzu mu zamu wuce da ita Apartment din Aydaaannnnn , ku da kuka Hajiya Rahina kwa sanar mawa da Hajiya Barmani Amaryar ta iso . Ammie tayi maganan tana kama Hannun Aaliyah tare da barin Su Hajiya Rahina nan a tsaye . Duk Abin da Aaliyah ke ji nasu bai ɓata mata rai ba don itama ba Auren take So ba . Kawai don yafi ƙarfin ta ne yayi mata fin karfi a cewan ta .  Tunanin Adda Hauwa ke sata kuka don ko sallama bata so sunyi ba tun wannan maganan da ta faɗa mata . Ina Son ki Adda , kuma zanyi biyayya a kalaman ki inshallah.....!
#Mmnteddy*🕊️SEXXI'ES HOUSE🕊️*
(Love and romantic story)

*Don Allah don darajar Allah ki taimake Ni kar ki fitar mun da Wannan littafi , kema Don Allah kar ki karanta mun Indai baki biyani Haƙƙi na ba , Idan kin karanta baki biyani ba Wallahi keda Allah , Don banga Tsadar shi ba da Zaki kasa cire kuɗi ki saya ,Indai kina iya siyan Data na WhatsApp ,to kam tabbas zaki iya cire ₦300 dai ki saya littafin The Sexxies House ƙaramin group kenan , Vip group₦500 SPC ₦1000 via 6037312299 Mohammed A'isha keystone bank ko katin MTN ta Wannan number 08081202932 .*

25

Ɓangaren Aydaan kuwa Kaman yanda suka saba zaune yake Wuraren yammacin ,tun da ya tabbatar da dai dole Aaliyah ta zama matar sa , wannan yasa shi sakewa duk wani masifar Hajiya Barmani dake yi akan yana ta Ɗoki kaman Wanda za'a kawo masa ƴar Gwal sam bai dame sa ba . Zaune suke a love Garden nasu , Ko wannen su da Abun da yake yi , Aydaaannnnn ne ya kalli Aaman tare da cewa " Aaman kuyi hakuri Duka ,duka haƙuri zamuyi ,wannan auren fa Hadin Hajiya Kaka ne , itace kawai da rigimar ta muna zaune lau ta jajubo mana . Numfasawa Aaman yayi kamin yace " Dama cikakkun mata zamu Aura duk Abin zai zo da Sauki , cousins Dina ,Ragowar mu duka . Shiru Aydaaannnnn yayi yana jin Zafin Tuno da Yanda Yake ganin Mubarak na sukuwa akan Sumayya ,amma yau gashi Wai itace zai Aura a

matsayin mata . Shi tun da yake bai taba Wani Abu da ita wai da sunan sex ba . Saboda tun da ya lura da ayyakun ta ya ja mata baya ,yau gashi Abun da yake gudu ya faru . Duk wai wa yafara Kawo Wannan Abun ne? . Aaman yayi maganan yana duban su duka , Lukman ne ya amshe da cewa " Kwaxin Mubarak mana ". Kallon Mubarak Aydaaannnnn yayi yana jin wani irin zafi da nadaman Abubuwan da suka aikata , sai kuma ya juyo tare da cewa " Mubarak muna ta magana but you keep silent ,baka ce komai ba sai charting da kake yi.   Ɗago da ido Mubarak yayi yana kallon su duka kamin ya taɓe baki yana cewa " please cool Okay?. Nine Wanda na fara kawo mana Shawarar mu yi wannan Abu ,don haka kar ku damu ,zan kawo mana mafita . Don mun yi Aure shikenan Sai ba zamu cigaba da kula Sauran babes Ɗin mu na Waje ba? Yanzu ne fah muke jin ƙuruciya a jikin mu ....Kaiiii ya isa da Allah malami.! Aydaan ya katse shi cike da Ɓacin Rai . Okay Naji kace haka , Ni duka ba Wannan tambayar muka yi maka ba. Maganan da nake shin kai ne Ka fara Kauda Budurcin Sumayya?. Eh ya akayi ? , girgiza Kai Aydaan yayi kamin yace " Okay Hibba fa? Humm itama Nine , Ummu Kulsum , Gyaɗa masa kai yayi alamun shine , Okay Ummi fa? Matar da Shi Mubarak ɗin zai Aura kenan . Wannan Aaman ne? . Saurin cewa Aaman yayi " A'a Ni bani bane , sai dai idan Lukman . Jin haka nan take Lukman ya amsa dashi ne . Yanzu to mu me kuka nufi akan mu? Kuna nufin Ragowar ku zan Aura ? . Aaman yayi maganan yana miƙewa tsaye don ransa yanzu ne ma yaji yana ƙara ɓaci . Mubarak ne ya kalli Shi kamin yace " Kaima kayi irin na ƙwazin Aydaan mana ,ka samu yar babyn ka wacce bata wuce 18 ba ka Aura ,kasan taste ba'a magana anan Wurin , idan kayi haka shikenan , kaga sai mu cigaba da Aikin mu , kaman yanda muka saba a baya. Kayi da ita da rana ,muyi da ita da dare .

